Cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance idan zai yi sallar Asuba sai ya zauna a wurin sallarsa har sai rana ta ɓullo tana ɗage

Jabir Ibnu Samura - Allah Ya yarda da shi -: Cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance idan zai yi sallar Asuba sai ya zauna a wurin sallarsa har sai rana ta ɓullo tana ɗage, kuma ya ce: Ya kasance ba ya tashi daga wurin da ya yi sallar Asuba har sai rana ta ɓullo, idan rana ta ɓullo sai ya tashi, kuma sun kasance suna tattaunawa sai su shiga labari cikin al'amarin Jahiliyya, sai su yi dariya shi kuma ya yi murmushi.

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Daga sunnar Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - cewa shi idan ya yi sallar Asuba sai ya zauna a wurin sallarsa har sai rana ta ɓullo a ɗage, kuma ya kasance ba ya tashi daga wurin sallarsa inda yakeyin sallar Asuba a ciknsa har sai rana ta ɓullo. Idan rana ta ɓullo sai ya tashi, kuma sun kasance suna tattaunawa sai su fara hira akan ambatan wasu daga cikin al'amuransu kafin Musulunci alhali shi ya yi shiru, sai su yi dariya wani lokaci kuma ya yi murmushi tare da su.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/65411